Rayuwa a Hanyar da Take Faranta wa Allah Rai (Sashe na 2)

An ɗauko daga babi na 12 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?* za a iya samunsa a dandalin jw.org/ha.

MANUFA: Ka bincika abin da ka yi imani da shi da kuma dalilin da ya sa ka yi hakan, kuma ka bincika abin da Littafi Mai Tsarki ya koyar don ka iya bayyana wa wasu abin da ka yi imani da shi.

SHIN, ZAI YIWU MU FARANTA WA ALLAH RAI DUK DA IRIN JARRABAR DA SHAIƊAN YAKE KAWO MANA?

1 KA BINCIKA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

Me ya sa wasu mutane za su iya ce a'a?

Me ya sa wasu mutane za su iya ce e?

Me *ka* yi imani da shi?

Me ya sa ka yi imani da hakan?

www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

2 KA BINCIKA ABIN DA LITTAFI MAI TSARKI YAKE KOYARWA

Ayuba, wani mutum mai aminci, ya jimre dukan masifun da suka faɗo masa.
(Ka duba babi na 12, sakin layi na 6-12 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

Karanta Ayuba 1:10, 11.
Mene ne Shaiɗan ya yi don ya sa Ayuba ya ɓata dangantakarsa da Allah?

_____

_____

_____

Karanta Ayuba 1:22; 27:5.
Mene ne Ayuba ya yi sa'ad da Shaiɗan ya jarraba shi?

_____

_____

_____

Idan saiwar itace ta shiga ƙasa sosai, da wuya guguwa ta ka da itacen. Hakazalika, idan dangantakarmu da Jehobah ta yi danƙo sosai, zai yi mana sauƙi mu jimre matsaloli

www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

Shaiɗan yana so ka daina bauta wa Jehobah, amma da taimakon Jehobah, za ka iya jimrewa.

(Ka duba babi na 12, sakin layi na 13-16 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

Karanta Misalai 24:10 da 1 Bitrus 5:8.

Ta yaya muka san cewa Shaiɗan zai iya jarraba mu kai tsaye (alal misali, ta wurin tsananta mana) ko kuma ya jarraba mu da wayo (alal misali, zai iya sa mu yi sanyin gwiwa) don ya ɓata dangantakarmu da Allah?

Karanta Ayuba 42:12-17 da Misalai 27:11. (Ka duba hoto na farko.)

Ta yaya muka san cewa Jehobah yana murna a duk lokacin da muka riƙe amincinmu?

Ta yaya sanin cewa shawarar da muka yanke zai iya faranta wa Jehobah rai yake shafanmu?

www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

3 KA BAYYANA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

IDAN WANI YA CE…

Idan mutum yana fuskantar matsaloli, hakan yana nuna cewa ya yi wani zunubi ne.

ZA KA IYA CE…

Mutane da yawa za su iya yarda da wannan maganar. Amma ni ban yarda ba domin…

_____

_____

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

_____

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

_____

IDAN WANI YA CE…

Tun da yake Allah ne mai iko duka, babu wani abu da 'yan Adam za su yi da zai dame shi.

ZA KA IYA CE…

Gaskiya ne cewa Allah ne mai iko duka. Amma na san cewa za mu *iya* faranta masa rai domin…

_____

_____

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

_____

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

_____

www.jw.org/ha © 2016 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania